مكتب الدعوة والإرشاد بالمعذر وأم الحمام



بالـلغة الهوسا

# معنى شهادة لا إله إلا الله

# MA’ANAR KALMAR SHAHADA.


FASSARA
ALIYU MUHAMMAD SADISU
DUBAWA
ATTAHIRU BILADIKKO

ترجمة
علـي محمـد سـادس
مراجعة
الطاهـر بـلا ديكـو



المكتب التعاوني للدعوة والإرشاد وتوعية الجاليات بالمعذر وأم الحمام

معنى شهادة لا إله إلا الله

# MA’ANAR KALMAR SHAHADA.

Fassarar:

***Aliyu Muhammad Sadisu***

***aliyusadis@gmail.com***

*Da sunan Allah mai yawan rahama mai yawan jinkai.*

**Ma’anar**: لا إله إلا الله (wato Kalmar shahada) babu abin bauta da cancanta sai Allah, wannan kuwa ya kunshi kore allantaka ga duk wani wanda ba Allah ba, ita ce bauta wa Allah da tabbatar da ibadar ga Allah shi kadai ba shi da abokin tarayya.

Bai halatta mu ce ma’anarta ita ce: Babu mahalicci sai Allah, ko babu mai ikon kagar wani abu sai Allah, ko babu wani da yake samamme sai Allah, saboda:

**Abu na farko:** Su kafiran Kuraishawa mushirikai a tun zamanin jahiliyyah ba sa cewa ba mahalicci sai Allah, ko kuma ba mai karfin iko a kan kagar al’amura sai Allah, Allah madaukakin sarki yana cewa:

﴿وَلَئِن سَأَلْتَهُم مَّنْ خَلَقَ السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضَ لَيَقُولُنَّ اللَّهُ قُلِ الْحَمْدُ لِلَّهِ﴾ لقمان: ٢٥

**Ma’ana:** “Kuma har idan ka tambayesu ‘Wa ya halicci sammai da kasa?’ tabbas za su ce maka Allah ne”. Suratu Lukman, aya ta: 25.

**Na biyu:** Lalle su kafiran Kuraishawa a lokacin da Ma’aikin Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi ya ce da su: Ku ce: لا إله إلا الله

**Ma’ana:** Babu abin bautawa da cancanta sai Allah.” Sai suka fadi abin da Allah madaukakin sarki ya ba mu labarinsa:

﴿أَجَعَلَ ٱلْـَٔالِهَةَ إِلَٰهًا وَٰحِدًا ۖ إِنَّ هَٰذَا لَشَىْءٌ عُجَابٌ ۝٥﴾ ص: ٥

**Ma’ana:** “Yanzu sai a sanya ababen bauta su koma abin bauta daya? Lallai wannan wani abu ne mai ban mamaki”. Suratu Sad, aya ta: 5.

Shin sun fahimci cewa da aka ce su ce: لا إله إلا الله cewa babu mahalicci sai Allah ko kuma babu mai iko a kan kagar al’amura sai Allah?. Amsa a nan ita ce: A’a, domin su din ba su yi musun hakan ba, abin da suka yi musunsa shi ne gabadayan ibada ta kasance ta Allah ce shi kadai, ba shi da abokin tarayya. Wannan ko ya nuna mana ma’anar: لا إله إلا الله ita ce babu abun bautawa da cancanta sai Allah.

## Rukunan Kalmar shahada: لا إله إلا الله

Kalmar shahada wato لا إله إلا الله tana da rukunai guda biyu:

**Rukuni na farko:** Korewa, wato kore duk wani abu da ya shafi Allantaka ga wani wanda ba Allah ba a cikin dukkanin halittun Allah, wannan ko ya fito a inda ka ce: لا إله ‘Laa ilaaha’.

**Rukuni na biyu**: Tabbatarwa, shi ne kuwa tabbatar da Allantaka da ibada ga Allah shi kadai, ban da wani wanda ba shi ba, wannan ko ya fito ne a inda ka ce: إلا الله ‘ Illallahu’.

## Sharuddan Kalmar Shahada: لا إله إلا الله

Ita Kalmar shahada لا إله إلا الله tana da sharudda guda bakwai:

**Sharadi na farko:** Ilimi/Sani. Abin da ake nufi shi ne sanin ma'anarta, korewa da kuma tabbatarwa, wanda hakan shi ke kore jahilcin ma'anarta, Allah madaukakin sarki yana cewa:

﴿ فَٱعۡلَمۡ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا ٱللَّهُ ﴾ محمد: ١٩

**Ma'ana:** "Ka sani, yadda al'amarin yake babu abin bautawa da cancanta sai Allah". Suratu Muhammad, aya ta: 19. Da kuma fadin Ma'aikin Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi: "Duk wanda ya mutu yana mai sane da cewa babu abin bautawa da cancanta sai Allah wannan, ya shiga aljanna".

**Sharadi na biyu**: Yakini watau sakankancewa shi ne wanda yake korar shakka, abin nufi shi ne ya kasance ya fadeta ne da yakini na abin da wannan *Kalmar* take nuni, wanda yake tabbataccen yakini ne. Domin shi imani babu abin da yake wadatarwa sai ilimi na yakini ba zato ba, to ta yaya za a ce yana da imani a lokacin da yake kokonto. Allah madaukakin sarki yana cewa:

﴿ إِنَّمَا ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ ثُمَّ لَمۡ يَرۡتَابُواْ وَجَٰهَدُواْ بِأَمۡوَٰلِهِمۡ وَأَنفُسِهِمۡ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِۚ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلصَّٰدِقُونَ ١٥ ﴾ الحجرات: ١٥

**Ma'ana:** "Abin sani kawai su Muminai, su ne wadanda suka yi imani da Allah da Manzonsa sannan ba su yi shakku ba, kuma su ka yi jihadi da dukiyoyinsu da kawunansu domin daukaka addinin Allah, wadannan su ne tsantsar masu gaskiya". Suratul hujurat, aya ta: 15. Sai Allah ya sa sharadin imanin nasu da Allah da Manzonsa kasancewarsu ba su yi shakku, amma wanda yake da kaikayi a zuciya a kan imani wannan yana cikin munafikai ne, Allah ya tsare mu, Allah madaukakin sarki yana cewa:

﴿ إِنَّمَا يَسْتَـْٔذِنُكَ ٱلَّذِينَ لَا يُؤْمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلْيَوْمِ ٱلْـَٔاخِرِ وَٱرْتَابَتْ قُلُوبُهُمْ فَهُمْ فِى رَيْبِهِمْ يَتَرَدَّدُونَ ﴿٤٥﴾ ﴾ التوبة: ٤٥

**Ma'ana:** "Abin sani kawai masu neman izininka su ne wadanda ba su yi imani da Allah da kuma ranar karshe ba, zukatansu suna kaikayi su kuma a cikin wannan kaikayin suke ta kai-komo". Suratut Taubah, aya ta:45.

**Sharadi na uku: Karba.**

Dole ne mutum ya karbi dukkanin abin da wannan *Kalmar* take kunshe da shi da zuciyarsa da kuma harshensa, hakika Allah ya labarta mana cikin labarukan wadanda suka gabata na yadda ya tserar da wanda ya karbi wannan *Kalmar*, da kuma ukubar wanda ya ki karbarta ya juya mata baya, kamar yadda ya ce:

﴿ إِنَّهُمْ كَانُوٓا۟ إِذَا قِيلَ لَهُمْ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا ٱللَّهُ يَسْتَكْبِرُونَ ﴿٣٥﴾ وَيَقُولُونَ أَئِنَّا لَتَارِكُوٓا۟ ءَالِهَتِنَا لِشَاعِرٍ مَّجْنُونٍ ﴿٣٦﴾ ﴾ الصافات: ٣٥ - ٣٦

**Ma'ana**: Lallai su sun kasance idan aka ce da su: Babu abin bautawa da cancanta sai Allah sai su yi girmankai. Sai su dinga cewa ; yanzu mu za mu bar allolinmu domin wani mawaki mara hankali". Suratus Saffat, aya ta: 35-36. Sai Allah madaukakin sarki ya sanya musabbabin yi musu azaba shi ne girmankansu na kin fadin: لا إله إلا الله wato babu abin bautawa da cancanta sai Allah, da kuma yadda suka karyata wanda ya zo da kalmar shahadar, ba su kore abin da ta kore ba kuma ba su tabbatar da abin da ta tabbatar ba, sai dai kawai saboda tsabar kin yarda da kuma girman kai suka ce:

﴿ أَجَعَلَ ٱلْـَٔالِهَةَ إِلَٰهًا وَٰحِدًا ۖ إِنَّ هَٰذَا لَشَىْءٌ عُجَابٌ ﴿٥﴾ ﴾ ص: ٥

**Ma'ana:** "Yanzu sai a sanya ababan bauta su koma abin bauta daya? Lallai wannan wani abu ne mai ban mamaki". Suratu Sad, aya ta: 5.

**Sharadi na hudu**: Sallamawa. Shi ne mutum ya sallama duk abin da wannan Kalmar ta yi nuni a kai, wanda hakan yake kore kin sallamawa hakan, Allah madaukakin sarki yana cewa:

﴿ وَأَنِيبُوٓاْ إِلَىٰ رَبِّكُمۡ وَأَسۡلِمُواْ لَهُۥ ﴾ الزمر: ٥٤

**Ma'ana**: Kuma ku mai da komai naku ga Ubangijinku kuma ku sallama masa". Suratuz Zumar, aya ta:54. Kuma Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ وَمَنۡ أَحۡسَنُ دِينٗا مِّمَّنۡ أَسۡلَمَ وَجۡهَهُۥ لِلَّهِ وَهُوَ مُحۡسِنٞ ﴾ النساء: ١٢٥

**Ma'ana:** Babu wanda ya fi kyawun addini kamar wanda ya sallama fuskarsa ga Allah yana mai kyautatawa". Suratun Nisai, aya ta: 125.

**Sharadi na biyar :** Gaskiya, wanda ke kore karya, shi ne ya fadi wannan kalma ta shahada da gaske tun daga zuciyarsa, kuma zuciyar ta yi daidai da harshensa, Allah madaukakin sarki yana cewa:

﴿ الٓمٓ ۝١ أَحَسِبَ ٱلنَّاسُ أَن يُتۡرَكُوٓاْ أَن يَقُولُوٓاْ ءَامَنَّا وَهُمۡ لَا يُفۡتَنُونَ ۝٢ وَلَقَدۡ فَتَنَّا ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۖ فَلَيَعۡلَمَنَّ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ صَدَقُواْ وَلَيَعۡلَمَنَّ ٱلۡكَٰذِبِينَ ۝٣ ﴾ العنكبوت: ١ – ٣.

**Ma'ana:** "Allah shi ya bar wa kansa sani. Shin mutane suna zaton a kyalesu don sun ce; Mun yi imani, alhalin su ba za a jarrabasu ba. Hakika mun jarrabi wadanda suka zo kafin su, to Allah zai bayyana wadanda suka gaskata kuma zai bayyana makaryata". Suratul Ankabut, 1-3.

**Sharadi na shida:** Yi domin Allah, wanda yake shi ne tsarkake aiki da kyakkyawar niyya daga dukkan abin da ya shafi guggubin shirka, Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ أَلَا لِلَّهِ ٱلدِّينُ ٱلۡخَالِصُ ﴾ الزمر: ٣

**Ma'ana:** "Ku saurara, tsaftataccen addini na Alla ne kadai". Suratuz Zumar, aya ta: 3. Kuma Alllah madaukakin sarki ya ce:

﴿ وَمَآ أُمِرُوٓاْ إِلَّا لِيَعۡبُدُواْ ٱللَّهَ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ ﴾ البينة: ٥

**Ma'ana:** "Kuma ba a umarce su da komai ba sai dai su bauta wa Allah suna masu tsaftace addini domin shi". Suratul Bayyina, aya ta: 5.

**Sharadi na bakwai:** So, Son wannan kalma ta shahada da son duk abin da Kalmar ta yi nuni a kan shi, da son wadanda suke bin Kalmar masu aiki da ita wadanda suke bin sharuddanta sau-da-kafa, da kuma kin duk wanda ya warware wannan bayani, Allah madaukakin sarki yana cewa:

﴿ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يَتَّخِذُ مِن دُونِ ٱللَّهِ أَندَادٗا يُحِبُّونَهُمۡ كَحُبِّ ٱللَّهِۖ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَشَدُّ حُبّٗا لِّلَّهِ ﴾ البقرة: ١٦٥

**Ma'ana:** "Kuma akwai daga cikin mutane wadanda suka rike wasu koma bayan Allah suna son su kamar yadda suke son Allah, wadanda suka yi imani sun fi son Allah a kan kowa". Suratul Bakara, aya ta: 165.

**Falalar Kalmar shahada لا إله إلا الله da kuma muhimmancinta.**

1. Ita ce mafi girman ni'ima da Allah mai girma da daukaka ya azurta bayinsa da ita, ta yadda ya shiryar da su ita, saboda haka ne ma ya ambace ta a Suratun Nahli, wacce take ita ce surar ni'imomi,

sai kuma Allah ya gabatar da ita kan kowace ni'ima, Allah madaukakin sarki yana cewa:

﴿ يُنَزِّلُ ٱلْمَلَٰٓئِكَةَ بِٱلرُّوحِ مِنْ أَمْرِهِۦ عَلَىٰ مَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦٓ أَنْ أَنذِرُوٓا۟ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنَا۠ فَٱتَّقُونِ ﴿٢﴾ ﴾ النحل: ٢

**Ma'ana:** "Yana sassaukar da Mala'iku da Ruhi (Mala'ika Jibrilu) da umarninsa ga wanda ya ga dama cikin bayinsa a kan ku yi gargadi yadda lamarin yake; Babu abin bautawa da cancanta sai ni, saboda haka ku ji tsorona". Suratun Nahli, aya ta: 2.

2. Ita ce babbar igiya mai karfi, wacce Allah madaukakin sarki ya ambata a fadarsa:

﴿ فَمَن يَكْفُرْ بِٱلطَّٰغُوتِ وَيُؤْمِنۢ بِٱللَّهِ فَقَدِ ٱسْتَمْسَكَ بِٱلْعُرْوَةِ ٱلْوُثْقَىٰ لَا ٱنفِصَامَ لَهَا ۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿٢٥٦﴾ ﴾
البقرة: ٢٥٦

**Ma'ana:** "To duk wanda ya kafurce wa dagutu kuma ya yi imani da Allah to hakika ya yi ruko da igiya mai karfi da ba za ta taba tsinkewa ba, kuma Allah mai ji ne kuma masani ne".

3. Ita ce alkawarin da Allah mai girma da daukaka ya ambata, a inda yake cewa:

﴿ لَّا يَمْلِكُونَ ٱلشَّفَٰعَةَ إِلَّا مَنِ ٱتَّخَذَ عِندَ ٱلرَّحْمَٰنِ عَهْدًا ﴿٨٧﴾ ﴾ مريم: ٨٧

**Ma'ana:** "Ba sa mallakar ceto sai dai wanda ya riki alkawari a wurin Allah". Suratu Maryam, aya ta: 87. Abdullahi bin Abbas ya ce: Alkawari shi ne shaidawa babu abin bautawa da cancanta sai Allah, kuma ya barranta zuwa ga Allah da duk wata dabara da wani karfi

sai dai ga Allah kadai, kada ya kaunaci kowa sai Allah madaukakin sarki.

4. Ita ce Kalmar gaskiya, kamar yadda Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿إِلَّا مَن شَهِدَ بِٱلْحَقِّ وَهُمْ يَعْلَمُونَ ﴿٨٦﴾﴾ الزخرف: ٨٦

**Ma'ana:** "Sai dai wanda ya shaida da gaskiya, kuma suna sane". Suratuz Zukhruf, aya ta: 86.

5. Ita ce Kalmar tsoron Allah, wacce Allah ya ambaceta a zancensa:

﴿وَأَلْزَمَهُمْ كَلِمَةَ ٱلتَّقْوَىٰ وَكَانُوٓا۟ أَحَقَّ بِهَا وَأَهْلَهَا﴾ الفتح: ٢٦

**Ma'ana**: "Kuma ya lizimta musu Kalmar tsoron Allah, kuma sun kasance su suka fi cancanta da ita kuma su ne iyalanta". Suratul Fath, aya ta: 26.

6. Ita ce tabbatacciyar Magana, Allah madaukakin sarki yana cewa:

﴿يُثَبِّتُ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ بِٱلْقَوْلِ ٱلثَّابِتِ فِى ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا وَفِى ٱلْـَٔاخِرَةِ﴾ إبراهيم: ٢٧

**Ma'ana:** "Allah yana tabbatar da wadanda suka yi imani da zance wanda yake tabbatacce a rayuwar duniya da kuma lahira". Suratu Ibrahim, aya ta: 27.

7. Ita ce dalilin samun aljanna da kuma tsira daga wuta.

﴿فَمَن زُحْزِحَ عَنِ ٱلنَّارِ وَأُدْخِلَ ٱلْجَنَّةَ فَقَدْ فَازَ﴾ آل عمران: ١٨٥

**Ma'ana**: "Duk wanda aka nisantar da shi daga wuta aka kuma shigar da shi aljanna to hakika wannan ya rabauta". Ali Imran, 185.

Kuma kamar yadda a hadisin da Bukhari da Muslim suka ruwaito: *"Duk wanda ya shaida da babu abin bautawa da cancanta sai Allah, kuma lalle Annabi Muhammad bawansane kuma manzonsa ne, kuma lalle Annabi Isa bawan Allah ne kuma manzonsa ne, kuma kalmarsa ce da ya jefa ta ga (Nana) Maryam, kuma raine daga gareshi, kuma aljanna gaskiya ce, kuma wuta gaskiya ne, Allah zai shigar da shi aljanna a kan aikin da ya kasance"*.

8. Ita ce babban dalili da ke hana dawwama a wuta ga wanda ya cancanci shiga wutar, kamar yadda yake a hadisin da ya yi Magana a kan ceto: Ku fitar da duk wanda ya ce: لا إله إلا الله daga cikin wuta, wato babu abin bautawa da cancanta sai Allah, kuma ya kasance a zuciyarsa akwai abinda ya kai nauyin kwayar komayya na imani.

Wadanda suke da لا إله إلا الله ko da sun shiga wuta saboda gazawar sauke hakkinta to watan-wata rana za su fita daga wutar, kamar yadda yake a hadisin Bukhari da Muslim: " Zai fita daga wuta duk wanda ya ce: لا إله إلا الله a zuciyarsa akwai wani alheri da ya kai nauyin silin gashi, kuma zai fita daga wuta duk wanda ya ce: لا إله إلا الله kuma a zuciyarsa a kwai abinda ya kai nauyin kwayar hatsi na alheri, kuma zai fita daga wuta duk wanda ya ce: لا إله إلا الله kuma a zuciyarsa akwai abinda ya kai nauyin kwayar komayya na alheri.

9. Lalle duk wanda ya fadi wannan kalma domin neman yardar Allah, to lalle Allah yana haramta shi ga wuta, kamar yadda hakan yake a hadisin Itban wanda Bukhari da Muslim suka ruwaito, lallai Allah tabbas ya haramta wuta ga duk wanda ya ce: لا إله إلا الله yana neman yardar Allah da hakan.

10. Saboda ita ce aka halicci aljan da mutum, Allah madaukakin sarki yana cewa:

﴿ وَمَا خَلَقْتُ ٱلْجِنَّ وَٱلْإِنسَ إِلَّا لِيَعْبُدُونِ ﴾ الذاريات: ٥٦

**Ma'ana:** "Ban halicci aljan da mutum ba sai domin su bauta mini". Suratuz Zariyat, aya ta: 56.

11. Ita ce hanyar samun tsira a duniya da kuma lahira, Allah madaukakin sarki yana cewa:

﴿ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَلَمْ يَلْبِسُوٓاْ إِيمَٰنَهُم بِظُلْمٍ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمُ ٱلْأَمْنُ وَهُم مُّهْتَدُونَ ﴾ الأنعام: ٨٢

**Ma'ana:** "Su ne wadanda suka yi imani kuma ba su rufe imanin nasu da zalunci ba wadannan suna da aminci kuma su ne shiryayyu". An'am, 82.

13. Ita ce farkon wajibi ga wanda aka dorawa hukunce-hukncen shari'a, Ma'aikin Allah tsira da amincin Allah su tabba a gare shi ya ce: "An umarce ni in yaki mutane har sai sun shaida da babu abin bautawa da cancanta sai Allah.

14. Ita ce wajibi na karshe ga wanda aka dora wa hukunce-hukncen shari'a, domin duk wanda Kalmar ta zama ita ce karshen maganarsa a nan duniya ya shiga aljanna, kamar yadda yake a hadisin Mu'az Allah ya kara masa yarda, duk wanda karshen maganarsa ta zama **لا إله إلا الله** ya shiga aljanna.

15. Ita ce wacce saboda ita aka aiko manzanni, kuma aka saukar da littattafai:

﴿ وَمَآ أَرْسَلْنَا مِن قَبْلِكَ مِن رَّسُولٍ إِلَّا نُوحِيٓ إِلَيْهِ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنَا۠ فَٱعْبُدُونِ ﴾ الأنبياء: ٢٥

**Ma'ana:** "Ba mu taba aiko da wani Manzo ba kafin kai face sai mun yi wahayi zuwa gare shi cewa babu wani abin bautawa da cancanta sai Ni, saboda haka ku bauta miNi". Suratul Ambiya, aya ta: 25.

**Abubuwan Dake Warware Kalamar Shahada: لا إله إلا الله**

**Na daya:** Shirka a cikin bautar Allah madaukakin sarki; Allah madaukakin sarki yana cewa:

قَالَ اللَّهُ تَعَالَى: ﴿ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَغْفِرُ أَن يُشْرَكَ بِهِۦ وَيَغْفِرُ مَا دُونَ ذَٰلِكَ لِمَن يَشَآءُ ﴾ النساء: ١١٦، وَقَالَ تَعَالَى: ﴿ إِنَّهُۥ مَن يُشْرِكْ بِٱللَّهِ فَقَدْ حَرَّمَ ٱللَّهُ عَلَيْهِ ٱلْجَنَّةَ وَمَأْوَىٰهُ ٱلنَّارُ ۖ وَمَا لِلظَّٰلِمِينَ مِنْ أَنصَارٍ ﴿٧٢﴾ ﴾ المائدة: ٧٢.

***"Lallai Allah ba ya gafarta wa idan aka hada Shi da wani, Yana gafarta abin da bai kai haka ba ga wanda ya so"***. Suratun Nisa'i, aya ta: 116.

Kuma Allah ya ce: ***"Lallai yadda lamarin yake duk wanda ya hada Allah ya yi wa Allah shirka (ya hada shi da wani) to tabbas Allah ya haramta masa aljanna kuma makomarsa wuta ce, azzalumai ba su da mataimaka".*** Suratul Ma'idah, ya ta: 72.

Yana kuma daga cikin shirka: Rokon mamata da neman agajinsu da yi musu yanka da alwashi.

**Na Biyu:** Duk wanda ya sanya tsani tsakaninsa da Allah, yana kiran wannan tsanin yana rokonsu ceto yana kuma dogara a kansu, (to wannan) ya kafirta, babu wani sabani.

**Na Uku:** Duk wanda bai kafirta mushirikai ba ko kuma ya yi kokonton kafircinsu ko kuma ya inganta ra'ayinsu (to wannan shi ma ya kafirta).

**Na Hudu:** Duk wanda ya kudurce a zuciyarsa cewar sabanin karantarwar Annabi (tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi) shi ne abu mafi cika a kan shiriyarsa, ko kuma hukuncin wannan din ne mafi kyau a kan hukunce-hukuncen Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi, kamar dai wadanda suke fifita hukunce-hukuncen dagutai a kan hukunce-hukuncen Ma'aikin Allah to wannan ya kafirta.

**Na Biyar:** Duk wanda ya yi fushi da abinda Ma'aikin Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi) ya zo da shi, ko da ko ya yi aiki da shi to ya kafirta, saboda Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ كَرِهُوا۟ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ فَأَحْبَطَ أَعْمَٰلَهُمْ ﴿٩﴾ ﴾ محمد: ٩

**Ma’ana:** “Abin da ya sa haka, saboda sun kyamaci abin da Allah ya saukar to sai Allah ya bata ayyukansu”. Suratu Muhammad, aya ta:9.

**Na Shida:** Duk wanda ya yi izgili da wani abu na addinin (musulunci) da manzon Allah (tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi) ya zo da shi, ko (izgili da) ladan da wannan abin ko ukubar wannan abin, to shi ma ya kafirta, dalili kuwa Allah madaukakin sarki yana cewa:

﴿ قُلْ أَبِٱللَّهِ وَءَايَٰتِهِۦ وَرَسُولِهِۦ كُنتُمْ تَسْتَهْزِءُونَ ۝٦٥ لَا تَعْتَذِرُوا۟ قَدْ كَفَرْتُم بَعْدَ إِيمَٰنِكُمْ ﴾ التوبة: ٦٥ – ٦٦.

Ma’ana: ***“ Kace; Yanzu Allah da ayoyinsa da kuma manzansa kuka kasance kuna izgili (da su)* Kada ku bada wani hanzari tabbas kun kafirce bayan imanin ku”.*** Suratul Taubah, aya ta: 65-66.

**Na Bakwai:** Asiri, kuma yana daga cikin nau’ukan asirin ***‘Kautarwa’*** wato a kautar da mutum daga abin da yake so yake bukata, kamar dauke hankalinsa daga ‘ya’yansa ko daga iyayensa ko daga mijinta ko daga matarsa. Haka kuma yana daga cikin nau’ukan sihiri ***‘Kimsawa’*** wato kimsa wa mutum abin da bai so a sa masa sonsa, to duk wanda ya aikata wannan ko ya yarda da shi to ya kafirta, dalili kuwa shi ne fadin Allah maigirma da daukaka:

﴿ وَمَا يُعَلِّمَانِ مِنْ أَحَدٍ حَتَّىٰ يَقُولَآ إِنَّمَا نَحْنُ فِتْنَةٌ فَلَا تَكْفُرْ ﴾البقرة: ١٠٢.

**Ma'ana:** ''Kuma ba sa koya wa kowa (sihiri) ballantana su ce abin sani kawai mu fitina ce kada ku kafirta''. Suratul Bakarah, aya ta: 102.

**Na Takwas:** Taimaka wa mushirikai da agaza musu a kan Musulmai, dalili kuma fadin Allah mai girma da daukaka:

﴿ وَمَن يَتَوَلَّهُم مِّنكُمْ فَإِنَّهُۥ مِنْهُمْ ﴾ المائدة: ٥١.

**Ma'ana:** ***''Duk kuma wanda ya jibincesu daga cikinku to lalle shi yana daga cikinsu''***. Suratul Ma'idah, aya ta: 51.

**Na Tara:** Duk wanda ya kudurce cewa; yana yiwuwa ga wasu daga cikin mutane su fita daga shari'ar Annabi Muhammad (tsira da amincin Allah su tabbata a gareshi), to wannan kafiri ne, saboda Allah madaukakin sarki ya ce:

﴿ وَمَن يَبْتَغِ غَيْرَ ٱلْإِسْلَٰمِ دِينًا فَلَن يُقْبَلَ مِنْهُ ﴾ آل عمران: ٨٥

**Ma'ana:** "Duk Wanda ya bi wani addini da ba Musulunci ba to ba za a taba karba daga wurinsa ba". Suratu Ali Imran, aya ta: 85.

**Na Goma:** Kau da kai daga addinin Allah madaukakin sarki, (shi) ba ya koyo ba kuma ya aiki da abin da addini ya koyar, dalili kuwa fadin Allah madaukakin sarki:

﴿ وَمَنْ أَظْلَمُ مِمَّن ذُكِّرَ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِۦ ثُمَّ أَعْرَضَ عَنْهَآ ۚ إِنَّا مِنَ ٱلْمُجْرِمِينَ مُنتَقِمُونَ ﴿٢٢﴾ ﴾ السجدة: ٢٢.

Ma’ana: ***’’Ba wanda ya kai girman zalunci kamar wanda aka fadakar da shi da ayoyin Ubangijinsa sannan ya kau da kai daga barinsu. Lalle mu dangane da fandararru muke daukar fansa’’***. Suratus Sajdah, aya ta: 22.

وَلاَ فَرْقَ فِي جميع هَذِهِ النَّوَاقِضِ بَيْنَ الْهَازِلِ وَالجْادِ وَالخَائِفِ إِلاَّ الْمُكْرَه، وَكُلُّهَا مِنْ أَعَظَمِ مَا يَكُونُ خطَرًا، وَمِنْ أَكْثَرِ مَا يَكُونُ وُقُوعًا فَيَنْبَغِي لِلْمُسْلِمِ أَنْ يحْذَرهَا وَيَخَافَ مِنْهَا عَلَى نَفْسِهِ.

A nan ba bambanci a kan dukkanin wadannan abubuwa tsakanin wanda ya yi su da wasa da kuma wanda yake da gaske da kuma mai tsoro sai dai kawai wanda aka tilasta masa, dukkanin wadannan suna da matukar hadari, kuma suna cikin abin da ake yawan aukawa cikinsu, saboda haka ya kamata ga dukkanin mutum musulmi ya kiyayesu kuma ya ji tsoronsu a kansa.

Muna neman tsarin Allah ya tsaremu daga abubuwan da suke haifar da fushinsa, da kuma zazzafar ukubarsa.

Tsira da amincin Allah su tabbata ga fiyayyen halittarsa Annabi Muhammad da iyalansa da kuma sahabbansa.


موقع المكتب على
خرائط Google

الحساب العام
SA 21 8000 0251 6080 1007 5881
حساب الوقف
SA13 8000 0251 6080 1017 7778

+966 11 488 4496
+966 11 482 7489
+966 55 0886 610
info@yaqeenweb.com
yaqeenweb
www.yaqeenweb.com